

Sanin Kalmar



Ina shaida wa Shaiɗan da kaina game da abin da Maganar Allah ta ce jinin Yesu yake yi mini (Rana 1)
Daga Derek Prince

Na gaskanta cewa Ubangiji ya nuna mani ta wurin fahimtar maganar Allah yadda za mu yi nasara a kan Shaiɗan. Yawancin Kiristoci sun san da cewa za mu iya yin nasara da shi ta wurin jinin Ɗan Ragon da kuma ta wurin shaidarmu. Amma da yawa sun mayar da ita Kalma ta maimaici kawai: "Jinin Yesu... Jinin Yesu." Ba wai ina son rage muhimancin wannan al'ada ba ne, amma na lura cewa wani lokaci wannan ba ya burge shaidan. A ganina dole ne mu yi amfani da wannan kalma da manufa.

Ta yaya za mu ci nasara da Shaiɗan ta wurin jinin Ɗan Ragon da kuma ta wurin shaidarmu? Akwai abubuwa uku da ke ciki:

1. Jinin Yesu;
2. Maganar Allah; kuma,
3. Shaidarmu.

Ga tawa fassarar yadda aka yi amfani da Ru'ya ta Yohanna 12:11: Muna yin nasara da Shaiɗan sa'ad da muka shaida da kanmu game da abin da Kalmar ta ce jinin Yesu yake yi mana.

A bayyane yake cewa idan za mu ba da shaida ga abin da Kalmar ta ce jinin yake yi mana, dole ne mu san abin da Kalmar ta ce jinin yake yi. A cikin makonni da yawa masu zuwa, za mu duba abin da Kalmar Allah ta ce jinin Yesu yake yi mana.

Ibada - Abincin Yini

Kwafi: WD-B097-001-HAU
Sabunta ta karshe: 18 Nov 2025
Yanar Gizo: derekprince.com/ha/resources


“Allah har yanzu yana ji da kyau. Yin tuba da watsar da zunuban mu yana sake bude hanya zuwa gare Shi.”
Derek Prince
derekprince.com/ha/resources
Cut here to use as a bookmark